# Allah ɗaya gari bamban al'adun ɗa suka shafi aure a kasar Nijar

Haruna Tankari
Issufu Abubakar
Bube Dobi

*Shekara 2004*

# Damagaram

Aure dai abu ne mai mahimmanci a ɓangare mai damar gaske. Kamar bisa kan fannin addini kowane iri ne a faɗin duniya. Sai dai yanda ake ɗaurin auren ya rabu. Don dai kowace jaha ko ƙabila da irin tasu al'ada.

A nan za mu bayyana yanda ake gabatar da aure a Damagaram. Wannan birnin ya ƙumshi hausawa kala biyu, da barebari, da sauran ƙabilu masu dama. Sai dai an fi sanin garin da hausawa. Ƴa magana kan cewa "duk ka yi tafiya ka tarda mutanen gari da wutsiya, kai ma sai ka nema ka sa ma kanka".

Da farko dai in za ka nemi auren yar musulmi, iyayen matar da kake nema za su nemi sani bisa kan addininka, da halayenka.

Sannan ka samu a ba ka izinin aiko mutanenka domin su kai sadaki, domin shi ne ƙafafun aure. Bayan an amshi kuɗin sadaki sai a rufe da yar fatiya.

Abin da ke biyo bayan sadaki shi ne lehe. Shi wannan lehe yana ƙumsar tufafi, kayan ado da sauransu, bakin ƙoƙarin mutum.

Lokacin da mata suka kawo lehe da kuɗin ɗumki, uwayen amarya su ma daga nasu ɓangare sai su fitar da la'adar yan aike.

Daɗa in ya so sai a sa ranar aure.

Ita dai amarya za ta shiga lalle, kwana huɗu, ko uku, ko biyu kafin ranar ɗaurin aure, amma sai in budurwa ce kuma daga wannan ranar za a soma karatun ƙur'ani, domin a sabke shi ranar da ake kai amarya gidan ango.

Ranar shiga lalle, dukan abukan amarya, yan uwa da dangi na haɗuwa gidan su amarya, domin wannan ranar a wurin waɗansu ta fi ranar ɗaurin aure. Kuma daga wannan ranar, amarya da wuya ta samu yini guda gidansu, sai dai a gari kamar gidan yan uwa da aminan arzikin ma'aifanta tare da garorinta.

Amarya na zaɓen gorori daga ɗaya zuwa biyu har gwargwadon yanda take so ; kuma duk nauyin

abincinsu da waɗansu yan buƙatunsu na bisa kan wuyan ango. Abin da za ya sa su cikin farin ciki har ranar ɗaurin aure.

Ita kuma babbar ranar ɗaurin aure, mafi yawan amare sun fi kasancewa a gidansu. Tun daga safiya ta waye ake soma shirye-shirye don saboda gidan amarya na karɓar baƙi masu zuwa ɗaurin aure.

Daga tawagar angaye ta iso, ba a jiran komi, sai a yi ta niyyar ɗaurin aure.

Idan aka gama ɗaurin aure, wani lokaci biki sai ya koma hannun mata, don dai su ne ke zarganiyar dafuwar abinci, da sauran hidimomi.

Lokacin da dare ya yi kamar bayan sallar ish'ai, abukan ango sai su sio da niyyar kai matarsu ɗakin abokinsu, inda take isko waɗansu yan kayayyakinta kamar su baliz, matala da sauransu, don dai tun da marece mata ke tafiya su gyara ɗaki.

Bayan an kai amarya gidan miji, har zuwa wani lokaci uwaye na yi mata gargaɗin zaman lafiya da mijinta.

Bayan kowa ya watse, sai a bar amarya da ango. Sai kuma washe gari a taru a kawo gara a yi gyaran ɗaki kitso da sauransu, da marece kuma su angaye sai su shirya wata babbar liyafa a cikin gidan amarya, waɗansu kuma na neman babban wurin walawa.

A ƙarshe sai fatan Allah ya ba da zaman lafiya da zuri'a ta gari wadda za ta bauta wa addinin Allah.

## Maraɗi

Shi dai aure kamar yadda kowa ya sani, ba abun wasa ba ne. Domin da farko dai sai an fara soyayya tsakanin sarmayi da budurwar da yake son aura. Kuma bayan haka akwai wata soyayya da uwaye suke haɗawa tsakanin ɗiyansu kamar ta ɓangaren su uwayen sarmayin su lura da cewa budurwar mai hankali ce, kuma tana girmama jama'a da sanin mutuncin kanta, da kuma asuli. Don ko a cikin alƙur'ani mai tsarki, ana bayani kan cewa da mutum in zai yi aure to ya zaɓi ma'abuciyar addinin isilama.

*Bayan* uwaye su haɗa su, kuma su kansu sun fahinci juna ta hanyar yin yan hiraraki, to sai uwayen budurwar su cewa sarmayin ya fito in da niyyar aure yake zowa. To a lokacin nan shi kuma sarmayin sai ya shaidawa uwayenshi.

A lokacin nan uwayen sarmayin sai su samu uwayen budurwar domin sun ɗan tattauna tsakaninsu.

To a yanzu sai a soma shirye-shiryen aure.

Da farko sai an ba da kuɗin sa ƙafa gidan su budurwar, da kuɗin na gani ina so, da sadaki, da akwati wanda ake sa kayan jiki, da takalma, da kayan kwalliya, da sabulu, da mai, da turare iri-iri da duk waɗanan abubuwa waɗanda mace za ta buƙata.

Bayan an sa ranar auren, ana saura sati guda ake sa amarya lalle. A cikin wannan satin ba ta zuwa ko'ina, ba ta yin aikin komi. Za ta zama kamar sarauniya. Da ruwan lalle za a yi mata murjen jiki har tsawon sati guda. Amma a cikin satin tana saduwa da ango da abokanshi don ƙara yin yan sauran shirye-shirye, kamar kiɗe-kiɗe wanda duk angon ne ke ɗaukar nauyin gabatar da su. Kuma a cikin wannan satin, kowane dare, kwana ake ana hira da raye-raye.

Sai ana gobe ɗaurin aure ne ake fitar da amarya daga lalle. Kuma ranar nan ce ake zuwa a sayo dabino, goro, a kuma shaidawa malaman da za

su ɗaura auren. A samo waliyai na amarya da na ango don su zama shaidu.

Bayan an gabatar da duk waɗannan shirye-shiryen, ranar ɗaurin aure sai jama'a sun taru ake shafa fatiya. Amma kahin a shafa fatiyar auren, sai an tambayi waliyin amarya a ce mishi: muna neman hannun wance an ba mu? Sai a ce mishi an ba ka. Za a yi irin wannan tambayar sau uku, kuma za a ba da amsar tambayar sau uku.

Bayan an ƙare ɗaurin aure, sai a ci-gaba da hidimar buki. Da dare ake kan amarya gidan mijinta. Amma kahin a kai ta, sai uwayenta da abokanta sun yi ta ba ta magana a game da yin haƙuri a halin rayuwar zaman aure.

In dare ya yi, sai a yiwa amarya wanka, a shirya ta tsaf, a yi mata kwalliya, a feshe ta da turare kala-kala a duk jikinta.

Sai a kuma sake yi mata nasiha da ta bi umurnin mijinta. Duk abin da ya ce ta yi, to ta yi shi, kuma duk wanda ya ce ta bari, to ta bar shi.

A cikin wannan lokacin ne angaye ke zowa da motoci ɗaukar amarya. Kahin angayen ke tafiya da ita, sai an kai ta wajen iyayenta ta nemi gafara, sannan sai yan rakiya su nufi da ita gidan mijinta, suna tafe suna waƙa. In an kai ta gidan miji sai a ƙara yi mata nasiha, sai kowa ya watse a bar ta daga ita abukiyarta, da abokin ango guda waɗanda su ma ke tafiyar su daga baya. In kowa da kowa ya watse, sai a yi kingin yar tsofuwa da za ta yi shimfiɗar kwanciyar ango da amarya.

Sai daɗa a bar amarya da ango sai da safe.

Daga an yi kiran sallar farin, wato da asuba, sai amarya ta yi gudu ta dawo gida, amma sai in ba taɓa tarawa da wani namiji ba. In ta zo gida uwayenta su yi ta murna, ana yi masu barka. In ko ba ta yi gudu ba, to ranar nan sai ɓacin rai ga uwayenta, kuma ba za ta samun darajar mijinta ba har abada.

Idan amarya ta yi gudu, ango na yi mata babbar kyauta kamar zinariya, ko kuɗi, ko kuma duk wani abu wanda za ya farinta mata rai.
Daga bayan yan gidansu sai su yi mata kitso, a ɗarma mata lalle, a yi dafe-dafe a maida ta gidan miji. A kuma kai mata kaya a gyara mata ɗakinta da kyau. Uwayen amarya sai kuma su lissafa kuɗin da ango ya kashe a maida mishi.

# Tawa

Aure sunna ce da ubangijinmu suba hanahu wata'ala ya umurce mu da yi. Yana ɗaya daga cikin sunnonin Annabi Mahamadu (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi).

Aure dai ya wajiba tsakanin namiji da mace.

Kowace ƙabila da yanda take gabatar da aure.

Auren adarawa abu ne mai kashin kuɗi. Idan mutum bai shirya ba, to ba za ya iya yin shi ba. A garin Tawa dai an ɗauka cewa, auren farko na ɗa namiji yana bisa kan uwayenshi. Saboda haka waɗansu uwaye suke zaɓa ɗiyansu matan da *suke* so. Kamar auren yana iya kasancewa auren gida. Waɗansu uwaye kuma suna ba ɗiyansu damar fiddo miji ko matar aure.

Idan sarmayi ya ga budurwar da yake so, sai ya gayawa wata yayarshi ko abukiyar uwarshi don ta shaidawa uwayenshi. Su kuma uwayen nashi sai su tura waɗansu mutane don su gayawa uwayen yarinyar da ɗansu na son auren ɗiyarsu.

Idan an ba da amsa, sai samarin ya tafi tare da abukanshi wurin hirar aure. Waɗansu da marece suke tafiya, waɗansu kuma da dare.

Cikin hira ne yarinya in ba ta son auren sai ta gaya masu, kuma in tana so sai ta gaya masu. Bayan sun ƙare hirar sai samarin su ba da kuɗin hira. Ana ba da jika biyar zuwa sama.

Daga baya kuma latijawa su kai kuɗin shiga gida, da ƙuɗin tambayar aure, sai kuma a tsaida ranar ɗaurin aure.

Ranar juma'a ce ake saurin ɗaura aure, da safe ko da marece bayan sallar la'asar.

Wurin ɗaurin auren wakilin ango za ya ba wakilin amarya sadaki (jika hamsin) da kuɗin sallama. In sun amince sai a raba goro ko dabino.

Ranar da aka ɗaura auren, yan matan amarya sai su tafi wurin angaye don amsar kuɗin shirye-shiryen biki.

Kamar in an samu kwanaki da ɗaura aure, sai a kaiwa amarya kaya iri-iri kamar atamfa, turare, mai.

Idan aka kai kayan shafin huri, sai a ba da ranar da za a kai lehe.

Amma ba duk uwayen amare ke saukin ba da rana ba. Sai uwar amarya ta shirya sosai, sannan a kai kayan amarya. Cikin kayan akwai na kakanni, na uwaye da na tabashinai. Ana kuma kai wasu kaya kamar (buta, fitila, lalle da sauransu), da kuma kuɗin uwar amarya da kuɗin yan matan amarya, waɗansu na kai har da kuɗin ɗunki.

Su kuma kayan ɗaki da uwar amarya ke ƙoƙarin ta shirya kafin aure ya tashi don har a yiwa ɗiyarta wulakanci, saboda kuma sun zama kamar al'ada, don dai in kaya ba su tafi ba, to amarya ba ta samun kwanciyar hankali.

Saboda haka dole ne uwar amarya ta yi kayan ɗaki.

Lokacin da aka kai lehe, sai a gayi ranar da za a sa amarya lalle da kuma ranar da za a biki (jiƙon lalle). Ana sa amarya lalle kamar sauran kwana biyar zuwa sati. Idan amarya ta shiga lalle,

ƙawayenta sai su tafi amsar kayan kuɗin zaman lalle. Ana sa amarya lalle tun da safe ko da marece bayan la'asar.

Wankan lalle shi kuma so biyu ake yi wa amarya shi safe da marece.

Marecen jiƙon lalle ƙawayen amarya suna tafiya wajen angaye su amso kuɗin abincin da za a dafa masu ranar biki. A ranar jiƙon lalle ne kuma uwayen amarya ke tafiya kan lalle gidan uwayen ango. Lallen cikin kwano ake kwaɓa shi a sa turare, in sun kai sai uwayen ango su sallame su. Su kuma yan matan amarya sai su kaiwa angaye abinci, su kai lallensu da faranti da za su ɗaura wa angaye lalle. In yan mata suka ɗaurawa angaye lalle, su kuma su ba su kuɗin halbe, kuɗin wankin faranti da sauransu.

Ga gobe a yi wa amaryar lalle da kalmisa.

Agayen su tura motar ɗaukar kayan amarya, suna cewa motar "uwar ɗiya mu ga ƙaryarki" ko uwar ɗiya kin shirya.

Mafi yawan aure zikiri ake yi, waɗansu kuma suna kiɗi. Bayan an gyara ɗakin amarya, sai a kai garar ango ta abinci da kuɗi, waɗansu suna kaiwa surinkinsu har jika ɗari uku. Idan ba a kaiwa amarya gara ba, to tana tare da tashin hankali kowane lokaci, har ma abin yakan kai ga rabuwar aure.

Idan dare ya yi sai angaye sun ba da kuɗi sannan ƙawayenta su fiddo amaryar ƙarya. Ita kuma amarya sai a kai ta gidan yar uwanta don su yi mata gargaɗi. Daga baya kuma a kai ta gidan surukanta don su ma su yi mata gargaɗi. Sai daɗa a kai amarya gidan ango.

Tsofin da suka kai ta da sauran mata sai su tafiyar su a bar amarya da ƙawayenta, su kuma angaye su zo. In dare ya yi sai su yi ban kwana. Da safe tsofuwar da ke yiwa amarya wankan lalle, ta tafi ta yi mata wankan lalle. Wannan ranar ita ce ake ce wa ranar zaman kalmisa. Kawayen amarya su yi mata dafuwa da safe da marece. Su kuma uwaye da rana suke tafiya don

su raba goronsu da kuɗinsu. A wannan ranar kaɗai ce ƙawayen amarya ke yini gidanta, ga gobe sai ta fara aikin gida.
Cikin kwana uku ko sati amarya sai ta koma gidansu, sai ace amarya ta yi gudu. Ago sai ya tura goro a rabawa mutane, ya kuma yi wa amarya babbar kyauta ta zinariya ko wani abu mai tsada.

# Tamaske

Aure abu ne mai mahimmanci da damar gaske wanda ya zama wajibi ga ɗan musulmi. Amma yanda ake aure ya kasu daban daban.
Ita dai wannan sunnar a karkararmu ta Tamaske ana rayar da ita kamar haka. Idan saurayi zai yi auren farin, ya wajabta ga uban da ya yi mishi, amma idan akwai hali. In ko babu hali, saurayin sai ya yi wa kanshi.
I ya ga budurwar da yake so, sai ya tura yarshi, ko ƙaunar ubanshi su faɗawa uban nashi. Idan ya kasance uban nashi ya yarda, sai a aika mutum biyu gidan su amaryar don zancen auren. Bayan *sun je* wurin uban yarinyar sai ya tambaye su zuri'arshi da addininshi. Bayan ya samu cikakkar amsa, sai ya ce to ranar da suka tashi su zo.
Bayan yan kwanaki, yan wajen su ango suna zowa da kayan lehe da kyauta. Ƴan gidan su amarya su ce masu, su tafi bayan sati biyu su zo amsar ranar aure. Kafin satin ya juyo, sai ango

ya kawo ma uwar amarya tsaraba don sanya amarya lalle.

Ranar sa lalle, sai yan uwa da abokanin arziki su taru gidan su amarya. Ana yin sa lalle har tsawon sati ɗaya. Da zaran an ƙare sa lalle, sai a sa ranar aure. Ranar ɗaurin aure da safe, malammai da wakilan aure, da shaidu su taru su ɗaura auren. Daga baya mata su ci-gaba da shagulgula da rana. In dare ya yi, sai a kai amarya gidan sarakunanta, sannan a isa da ita gidan angonta.

Kowa ya watse ya bar su daga ita sai ango. Da asubahin sai amarya ta dawo gidansu kitso. A yayin da ake kitson waɗansu daga cikin matan gari su je gyaren ɗakin amarya. Saura kuma su ci-gaba da dafe-dafen kaji. Da dare sai a ɗauki amaryar zuwa gidanta. K ta tafi, sai an gurfanar da ita a gaban ma'aifanta don neman gafara.

Bayan sun gafarta mata, sai kuma su sa mata albarka, gami da roƙon Allah ya ba ta albarkar aure.

# Tatsinniyoyi Hausa

# Ta farce

Akwai cikin wani ɗan gari, wata mace da bata taɓa samun aifuwa ba, kullum dai sai tata rokon allah ya ba ta ko ɗanɗa guda. Ana nan da watara na sai ɗan ƙurji ya hito mata da farce da ta fashe shi sai yan iya kyaukkyawa ba ta san abun da ya taɓa.

Wannan iya, kuma kowane irin aiki ne sai dai tayi ma kanta. Wata rana sai ta ce ma iyarta ta shiga rahewa ta ɗebo hatsi, sai ta ce ita bata shiga rahewa da nan uwar tata ta ce mata wane irin kyau ne gare ta da bata shiga rahewa ita ko ta ce sai taga wanda tahi ta kyau, ta kama hanya. Garin da duk ta kai sai ta tsaya ta ɗibi waha.

In shiga rahewa inna ta hana ni shiga rahewa abba ya hana ni shiga rehewa niko na ture in shiga rahewa in Sokoto in Kano, in birnin ba iro sai naga mai ƙoyon da ina da ƙayan da iro sai dan nan samari da yan mata sunka ce mata ta wuce gaba nan babu yarinya da ta kai ki kyau.

Kuma ta kai wani gari ta ɗibi waƙa anka ce ta tahi gaba, sai da ta kai inda adda mai kyaun garin, ta ɗibi waƙa, dan nan kowa ya hito yana kallon ta.

Akwai waɗansu samari guda uku dukan su yarinya guda suke so, ama dai kowanen su bai sani ba ; kuma basu taɓa gamuwa ba wajen hira. Wata rana wannan budurwar tahi niya tafiya wani ɗan gari, sai ta ce ma waɗannan samari guda gida uku su rakanyeta tun da safe duka uku suka tashi zuwa rakiya. Ana tsakan tahiya sai aka sako ruwa, sai guda cikin su ya ce mi zai yi ya tare waɗannan ruwa sai ya samu wata yar dubara, ya gina ɗaki ya ruheta da cawa sunka shiga sai da aka ɗoke ruwa, da ruwan sunka ida sai sunka gama hanya. Ana tsakar tahiya sai budurwan tahi talalaɓiya ta ɗauketa kayin ta kai ƙasa guda cikin su ya ɗobo icce ya janjera dan ka ta kai ƙasa.

Kuma suka kama hanya, sai gasu gaban wani babban tabki kuma hanya da za su bi ce, basu san ƙakan da za su yi su wuce, daga nan guda ya

ɗebo takobin shi ya raba ruwan tabki biyu suka samu suka wuce.

# Tatsinniyar Mahalbi

Wani mahalbi ne yake da ɗiya mai ɗan karan kyau.
Diyar ba ta fitowa waje, kullum gidansu rufe yake. Kuma babu wanda ya san sunanta «Delu» sai ubanta.
I ya tafi halbi sai ya kaso namomin daji da yawa. In ya zo gida sai ya ce:
Ke Delu, Dela, yar aifuwa maza Dela, buɗe mini gida na yo dare.
In ya yi wannan waƙar ya ƙare, sai ta buɗe mishi gida ya shiga. Kullum dai, haka ne; sai wata rana wani bafade ya laɓe jikin gidan. Da ya zo, ya yi waƙar da yake yi ya ƙare,sai Delu ta buɗe mishi gidan ya shiga. Wan safake sai bafade ya zo ya ce ma sarki: "ranka ya daɗe, na ga wani abu, in ba gidanka ba, gidana". Sarki ya ce "gidanka?" a'a «gidana».
Sai ya ce: na ga wata yarinya mai ɗan karan kyau gidan wani mahalbi.

Sarki ya ce to ku je ku kamota. Da suka tafi sai bafaden ya yi waƙar kamar yadda ubanta yake yi, ita kuma sai ta buɗe ƙofar gidan sai suka shiga suka kamata suka kai ta gidan sarki.

Da uban ya zo ya yi waƙa, ya yi waƙa ya ji shiru. Ko da ya taɓa ƙofa sai ya ga gidan buɗe yake. Ya yi ta kuka.

Kan ƙurus, kan kusu

Da muguwar rawa gwamma ƙin tashi.

Akwai wani sarki, shi dai wannan sarkin yana da wata jakada wanda ya amince da ita iyakar amincewa. Kuɗinsa ma duk ita ke ajewa. In yana son wani abu sai ya aika kawai ta bashi.
Suna nan haka kullum in anyi lissafin kuɗin sai a ga suna saurin ƙarewa.
In ya lissafta kuɗin duk abin da ya kashe cikin yini ya samu kamasfan biyu, in ya shigo ya tambayeta sai jakaduyar nan tace fan biyar ko shidda. Duk abin ya dami sarki amma bai bayyana mata ba don ya tabbata da dai ba ta daukar ko anini sai inya bata saboda haka ya ce daga yau zan amshi abinda zan yi amfani da shi a yini, a lokaci guda.

# Ambuka game da tuwo

Wata rana wani mutunene, shi dai wannan mutumin sunan sa Ambuka sai ya yi baƙo. To abune dai da yake cikin al'adu idan ka yi baƙo, ka yi mishi liyafa domin in yaje gida ya faɗa to game da haka nan, ya samu ya yi ƙokarin samo nama aka gyara masu dage-dage.

Lokacin abinci da ya zo sai ya tattaro ƙasussuwa ya kai gaban baƙo ya tara ƙashi mai tauri wato shi nufin shi baƙo na kan ƙashi ya na ɓata lokacinshi wajen gurgurza shi kuma ya sami tuwon da nama ya ci ya ƙoshi. Sai ya cewa baƙo. To ga wannan fa dan kai aka kawo. Sai baƙo ya ƙi shurarar shi ya ɗora cin tuwonsa. Ana nan, ana nan maigidan sai ya sami wani wayo sai ya zage hannun shi daga cikin kwano.

Shi ko baƙo sai cin tuwonshi ya ke wato shi nufushi, baƙo dai ya dena cin tuwo, idan an ɗauke an maida sauran gida shi ya ida kayanshi.

Baƙo ya yi kamar bai ji ba mutun dai ya ga tuwo yana ƙasa sai ko ya maido hannunsa ya ce kai in kai jaki ne ni ma jakin ne.

Dan shi ne ake cewa rewa bata da daɗi

## Abin da ke sa maciji na cin kwaɗo

A lokacin da, can da, kwaɗuna a cikin su ke da sarki, sarkin sauran namomin daji kamar su micizai da sauran su.

Don tsananin arzikinshi ba a san ba ma ko shanu nawa gare shi ba, balle awaki da sauransu.

Dan tsananin tsoron da ake mishi da kuma sai abin da ya ce wa mutanen nashi ke yi, duk masu mishi kiyo ba su iya tambaya shi alhakinsu ba.

Amman duk a cikin wadanda yake iko, duk ya hi rena micizai.

Kullum sa yake ana ba su kashi yadda ya kamata.

Kuma bayan an ba su kashin sai ya yi ta sa su wahala har su gaji gaba ɗaya. Amman duk wahalolin da yake ba su, ba su taɓa mishi rishin arziki ba.

Wata rana sai tsohuwar sarkin ta rasu. Daga ta kowane lungu, gudu suke don su zo, su nuna rishin jin daɗinsu.

Kwaɗo, duk da yana na gaban gawar uwarshi bai bar ƙuntata masu ba, sai biya yake layi-layi yana ba waɗanda ba su nan ga yin kuka kashi don kowa da kowa ya yi ta kukan.

Yana cikin ban kashin sai ga wani tsohon maciji a cikin wani lungu yana gyangyaɗi.

Nan da nan ya faɗa shi da bugu, sai yan uwan suka kama kuka don tsananin jin tsoro.

Sai wani ɗan ƙaramin miciji ya tashi ya ce duk waɗannan koke-koken da muke yi don nuna rishin jin daɗinmu bai isa ba ha sai ka shiga mutane da bugu, sai ko ya faɗa shi da bugu, da ya yi zuciya, sai kawai ya buɗe bakinshi ya haɗe kwaɗon, su kuma yan uwar nashi suka faɗa sauran.

Shi ne mafarin macizai ke cin kwaɗinan.

## Labarin wani malami

A wani ɗan gari ke da wani malami. Shi dai wannan malamin yana da mata uku.
Malam Zakari mai kirki ne. Amma abin da ke mashi ciwo da bai aifuwa. Saboda bai aifuwa matanshi suka tafi suka barshi. Daga shi sai almajirai. Akwai babban abokinshi, wannan abokin mai jin tausai ne. Sai ya ce zai ba malam Zakari ɗiya aure. Ya zo gidan malami dan ya shaida mishi.
Malam ya ce ka shaidama yarinya ne, da luwarta, da sauran yan uwa ? Abokin ya je gida ya shaidawa kowane cikinsu.
Da zuwa gida ya fara shaidawa ma uwar yarinya.Uwa ta ce. Wanda bai aihuwa za a aura wa Lami ? Sai mijin ya ce : komi na Allah ne, kin ka san na da rabo wajen ubangiji. Mata malam ta ce ka shawartawa wa Lami ? Ya kiro Lami bayan salar magariba ya gaya mata. Mi ya fito daga bakin Lami ? Ba komi baba abinda kuka ce shi za

a yi. Baban Lami ya yi murna. Ya ce ... Allah shi yi albarka. Bayan ya shawarta wa kowa, sai ya koma wayen malami ya gaya mishi. A ka zo aka yi buki, sai aka kai Lami gidan mijinta. Bayan wata uku sai Lami, ta fara ciwo kama su ciwon kai da sauransu. Ashe ciki ne ke ga Lami. Malami ya yi murna. Wata rana yana kwance bai da lafiya, ya kira matarshi ya ce kin ga wannan ciwon bai bari na a duniya, in kika aihu ɗa ko ɗiya ki rike su da amana. Kuma ki sa su makaranta, kamar yanda muka yi makaranta.

## Tsatsinniya : Biri, Kura, Bunsuru da Akuya

A cikin wani daji akwai wata kura wa'dda ke da gidanta mai kyau ƙwarai da gaske a wani kogo, ta gyara shi da kyau, babu abin da babu a ciki. Sai kurar nan ta samu wani biri ta sa shi tsaron gidanta, kullum in ba ta nan, don kar wani abu ya fasa, ko kuma a yi mata sata. Kullum biri nan ba ya rabuwa da gidan kura. Sai wata rana yana zaune sai ga wani bunsuru da matarshi da ɗiyansu uku. Sun faɗo gidan kura. Dalilin sun tafi kiwo har dare ya yi musu, suka rasa hanyar komawa gari. Suna tsoron kar su gamu da zaki ko kura. Biri ya ce musu ku rufa ma kanku asiri, gidan kura ne, kuma in ku kawo taurin kai, in je yanzu in gaya mata ta zo ta hau doronku ɗai-ɗai. Akuya ta cema mijinta ƙaƙa za muyi ? Biri ya ce ni fa na gaya muku, ka gudu, in ba haka ba zan je in kirawo ta. Sai bunsuru ya ce ka tafi, ka gaya mata masu gidan ne suka zo. Da biri ya tafi, bunsuru ya cema matarshi in muji tafiyar su, sai

ki tura ɗiyan nan cikin kogo, idan su fara kuka sai ki gaya mini ni kuma in tamboye ki mi suke so ? Daga nan sai ki ce naman kura danye suke so. Biri har ya kai wurin kura, ya gaya mata, ita kuma ta tsorata, har hankalinta ya tashi. Kura ta ce su tafi ta gansu, sun kusa kawowa sai suka ji akuya tana ce ma mijinta akwai kingin najiya yaran nan sun ƙi ci, sai naman kuru danye suke so. Koda kura ta ji haka, sai ta ce ma bari ya tafi ya gaya musu bai gan ta ba. Kura ta yi cikin daji. Biri ya tafi ya gaya musu. Su kuma suka samu gidansu.

# Tatsinniya : Zaki, biri da kura

Wata rana kura, zaki da biri suna neman abinci, sai kura ta ce ta iya sata. Zaki ya ce mata tun da kin iya ki tafi ki sato. Kura ta tafi ta sato ƙwai shidda da kaza shidda. Da ta dawo sai zaki ya ce ta raba ita da ta sato su. Kura ta ce tun da mu uku ne kowane ya ɗauki ƙwai biyu da kaza biyu. Zaki, shi kuma da ya ji kura ta gayi haka sai ya yi kwance kwance ya halbe ta ga ciki, ita kuma ba ta tsaya ɓata lokacin ta ba, sai ta ce ƙafa mi na ci ban baki ba. Shi biri ya haye bisa icce. Daga ranar nan kura ba ta ƙara dawowa ba cikin gari, shi guma biri kullum yana bisa icce.